# Shawarar DAC akan kawo ƙarshen Cutarwa, Cin Zarafi da Tursasawa ta fuskar Jima'i a Haɗin Kai Bunƙasa da Taimakon Agaji: Muhimman Rukunonin Kariya da Tallafawa



**OECD Legal Instruments**

BETTER POLICIES FOR BETTER LIVES

This document is published under the responsibility of the Secretary-General of the OECD. It reproduces an OECD Legal Instrument and may contain additional material. The opinions expressed and arguments employed in the additional material do not necessarily reflect the official views of OECD Member countries.

This document, as well as any data and any map included herein, are without prejudice to the status of or sovereignty over any territory, to the delimitation of international frontiers and boundaries and to the name of any territory, city or area.

This document is provided free of charge. It may be reproduced and distributed free of charge without requiring any further permissions, as long as it is not altered in any way. It may not be sold.

This is an unofficial translation. Although best efforts have been exercised in order to ensure correspondence to the original texts, the only official versions are the English and French texts available on the OECD website https://legalinstruments.oecd.org.

Ce document est publié sous la responsabilité du Secrétaire général de l'OCDE. Il reproduit un instrument juridique de l'OCDE et peut contenir des informations complémentaires. Les opinions ou arguments exprimés dans ces informations complémentaires ne reflètent pas nécessairement les vues officielles des pays Membres de l'OCDE.

Ce document, ainsi que les données et cartes qu'il peut comprendre, sont sans préjudice du statut de tout territoire, de la souveraineté s'exerçant sur ce dernier, du tracé des frontières et limites internationales, et du nom de tout territoire, ville ou région.

Ce document est fourni gratuitement. Il peut être reproduit et distribué gratuitement sans autre autorisation, pour autant qu'il ne soit pas modifié de quelque manière que ce soit. Il ne peut être vendu.

Ceci est une traduction non officielle. Bien que tout ait été mis en œuvre pour assurer la correspondance avec les textes originaux, les seules versions officielles sont les textes français et anglais disponibles sur le site Internet de l'OCDE https://legalinstruments.oecd.org.

Wannan wata fassara ce wadda hukumar basu amince da ita ba daga asalin ta Turancin, wadda Ƙungiyar Haɗin Kan Tattalin Arziki ta Duniya (OECD) ta wallafa. Waɗannan ƙungiyoyin ne suka fassara wannan wallafar da kansu: Social Development Direct da Translators without Borders. Ƙungiyar Hadin Kan Tattalin Arziki ta Duniya (OECD) ba su amince, kuma ba za su ɗauki alhakin ingancin da daidaituwar wannan fassarar ba.

**KWAMITIN OECD NA TAIMAKON BUNKASA (DAC),**

**GIRMAMAWA** Shawarar Tarayya akan Daidaituwar Jinsi a Ilimi, Ɗaukan aiki da Kasuwanci [OECD/LEGAL/0398]; Shawarar Tarayyar Haɗin Kai Bunƙasa akan Gudanar da Hatsarin Rashawa [OECD/LEGAL/0431]; Shawarar Tarayya akan Daidaituwar Jinsi a Rayuwar Jama'a ta yau da kullum [OECD/LEGAL/0418]; da Shawarar DAC akan Haɗin Taimakon agaji Bunƙasa-da Zaman Lafiya [OECD/LEGAL/5019];

**GIRMAMAWA** ga Sanarwar Gamayyar DAC Tidewater akan Shawo kan ci da gumi da Cin Zarafi ta Hanyar Jima'i a Ɓangarorin Aikin Bunƙasa da Taimakon Agaji da Shelar Kariya ga Fallasa daga Amfani da dama da Cin Zarafi ta Hanyar Jima'i a Taimakon Kasa da ƙasa da Ministocin Kawo Ci Gaba na G7 suka yi alkawari;

**GIRMAMAWA** ga alkawuran da masu bada kuɗin tallafi suka yi don magance ci da gumi da cin zarafi da tursasawa ta hanyar jima'i a ɓangaren aikin agaji na ƙasa da ƙasa a Taron Kariya na London a 2018;

**GIRMAMAWA** ga gidauniyar da bangaren kayayyaki daban-daban na ƙasa da ƙasa akan ɓangarori da yawa na daidaituwar jinsi da hakkokin bil'adama suka samar, musamman ka'idodin dake cikin Sanarwar Kasashen Duniya game da Hakkokin Yan-adam da wasu abubuwan da suka dace na Dokar Taimakon Agaji na Duniya har da Yarjejeniyar Geneva da dokoki don hakan; Yarjejeniyar Duniya akan Hakkokin Farar Hula da Siyasa; Yarjejeniyar Duniya akan Hakkokin Tattalin Arziki, Zamantakewa da Al'adu; Yarjejeniyar Majalisar Dinkin Duniya akan Hakkin Yara; Yarjejeniyar Majalisar Dinkin Duniya akan Kawar da dukkan nau'in Nuna Banbanci akan Mata; Yarjejeniyar Majalisar Dinkin Duniya akan Kawar da Tashin Hankali akan Mata (A/RES/48/104); Cikkaken Dabarun UN akan Taimako da Tallafawa Wadanda suka Tsira daga Cutarwa da Cin Zarafi ta Hanyar Jima'i daga hannun Ma'aikatan UN da Masu alaka (A/RES/62/214); Dokokin UN akan Zargin Cutarwa da Cin Zarafi ta Hanyar Jima'i da ya Shafi Abokan Aiki; Yarjejeniyar Babban Taron Majalisar Dinkin Duniya na 2018 akan Karfafa ƙoƙarin hana da shawo kan dukkan nau'in tashin hankali kan mata da 'yan mata: tursasawa ta hanyar jima'i (A/RES/73/148); da Yarjejeniyar Tarayyar Turai akan hana da magance tashin hankali akan mata da tashin hankali na cikin gida;

**GIRMAMAWA** ga alkawuran siyasa masu amfani da a yi la'akari da su cikin mahallin Majalisar Dinkin Duniya, gami da Ajenda ta 2030 don ci gaba; Shirin Aiki na 1994 na taron kasa da kasa akan Jama'a da Ci gaba; Shelar Beijing a 1995 da Dandalin Daukan Mataki na Taron UN na Duniya na Huɗu akan Mata da takardun sakamakon taron bitar su;

**GANO** cewa ci da gumi da cin zarafi ta hanyar jima'i (SEA) da tursasawa ta hanyar jima'i (SH) ba'a amince da su ba kuma suna sabawa ka'idodi da dokokin duniya da ta shafe su, kuma da cewa SEA da SH sun ƙunshi halaye da ba'a amince da su ba kuma suna iya haifar da mumunnan sakamako masu dorewa da rudewa ga mutane da al'umma da, inda masu aikin agaji suke aikatawa da abokan aikinsu, yana jawo tambaya akan ingancin al'umma masu taimakon agaji da sahihancin agajin kansa;

**GANO** cewa hatsarin SEA da SH na rage tasirin ƙoƙarin duniya don cimma manufofin 2030 na Ci gaba Mai Dorewa, musamman Manufar Ci-gaba Mai Dorewa ta Biyar (SDG) 5, "Samun nasara wajen daidaituwar jinsi da karfafawa dukkan mata da'yan mata gwiwa";

**GANO** cewa hatsarin SEA da SH na ƙaruwa idan masu ba da tallafi da abokan aikinsu sun kasa ƙafa al'adu da dabi'un ƙungiya wanda ke hana SEA da SH ko ɗauki mataki da wuri don gudanar da magance hatsarorin, har da hatsarorin da suke ƙaruwa sakamakon aiki a yanayin da babu tabbaci, rikici ya shafa kuma akwai yiyuwar rashin daidaituwar iko da jinsi su kasance a wajen;

**GANO** cewa masu bada kuɗin tallafi da abokan aikin su na buƙatar karfafa daidaituwa da haɗin kai wajen hana da magance matsalolin SEA da SH, samar da dandalin masu bada kuɗin tallafi mai karfi don jagoranci canjin al'adun ƙungiya da ɗaukan nauyi; taimakawa mai tsira-da wanda aka azabtar da magance rashin ɗaukan hukunci akan masu laifi; karfafa karfin fannin aikin agaji; gano muhimmiyar rawa da ƙungiyoyin hakkokin mata da ƙungiyoyin da mata suke jagoranta za su taka wajen hana da magance tashin hankali akan mata da 'yan mata, da buƙatar tabbatar da muhimman rawar da zasu taka a ƙoƙarin hana da magance SEA da SH na gida da na ƙasa da ƙasa; da kuma bin ka'idodin da suka dace na ƙasa da ƙasa don rage yiwuwa da tasirin SEA da SH daga ma'aikata da suke ba da taimakon agaji na ƙasa da ƙasa;

**GANO** ƙoƙarin UN don hana da magance SEA da SH, har da Rahoton Babban Sakatare akan Matakai na Musamman don Kariya daga ci da gumi da Cin Zarafi ta Hanyar Jima'i: Sabuwar hanya (2017); Mujallar Babban Sakataren UN: Matakai na Musamman don Kariya daga ci da gumi da Cin Zarafi ta Hanyar Jima'i (2003), Haramta nuna banbanci, tursasawa, har da tursasawa ta fuskar jima'i, da amfani da matsayi don cutarwa (2008), da Kariya daga ramakon gayya da kai ƙarar rashin da'a da kuma haɗin kai tare da binciken hukuma (2017); Yarjejeniyar Tarayyar Tsaro ta UN akan Mata, Zaman Lafiya da Tsaro, har da yarjejeniya 1325 (2000) da yarjejeniyar da aka yi daga baya zuwa kuma haɗe da Yarjejeniya 2242 (2015); Tsarin Ka'ida akan tursasawa ta hanyar Jima'i (2018); Har da ayyuka masu muhimmanci daga Shugaban UN na Musamman akan inganta tallafin UN zuwa SEA, Mai Goyan bayan Hakokkin wanda aka azabtar na UN, Asusun UN don wadanda suka tsira daga SEA, Yarjejeniyar Son kai tsakanin Babban Sakataren UN da ɗai-ɗaikum Jihohi, Tarayyar Shugabanni akan Kariya da magance ci da gumi da cin zarafi ta hanyar jima'i a ayyukan Majalisar Dinkin Duniya, Mashawarta 'kananan kungiyoyi masu zaman kansu akan hana ci da gumi da cin zarafi ta hanyar jima'i, da Ajandar Grand Bargain don 'Yancin bil'adama (2016); da dokar Shigar da Mutane masu Nakasa cikin Ayyukan Taimakon Agaji (2016);

**GANO** Ka'idodin Kwamitin Kungiya mai Jagorantar Kungiyoyin Agaji da Mafi Karancin Ka'idodi akan Kariya daga ci da gumi da Cin Zarafi ta Hanyar Jima'i (MOS-PSEA), da Muhimman Ka'idodin Aikin Agaji akan Inganci da Ɗaukan nauyi (CHS), a matsayin wajibni ka'idodi na ƙasa da ƙasa;

**GANO** muhimmancin haɗa hanyoyin da suke la'akari da mai tsira-da wanda aka azabtara cikin ka'idodi PSEA da SH, bisa ga ka'idodin masu jagorantar: (i) tsaro; (ii) sirri; (iii) daraja; da (iv) rashin nuna bambanci da aka bayyana a Cikkakun Dabarun UN akan Taimako da Tallafawa Masu tsira daga Cutarwa da Cin Zarafi ta Hanyar Jima'i ta hannun ma'aikatan UN da abokan aiki (A/RES/62/214), har da na yaran da aka azabtar na buƙatar kulawa musamman don tabbatar da tsaro, kariya da lafiyarsu;

**GANO** cewa SEA da SH suna da tushe sosai a tsarin rashin daidaito musamman rashin daidaituwar jinsi, wanda ke haifar da cin zarafi don banbancin jinsi, tare da sauran nau'in tashin hankali, da nuna banbanci;

**GANO** cewa SEA da SH sun ƙunshi sabawa da cin zarafin 'yancin dan Adam, don haka karfafawa, kariya da darajanta hakkokin bil'adama dole ya zama muhimmin abu a lokacin hana da magance SEA da SH. Tabbatar da hanya bisa ga 'yancin bil'adama wanda ba ya cutarwa a lokacin haɗin kai don ci gaba da ba da taimakon agaji na da matukar muhimmanci. Ana buƙatar kulawa musamman don gungun mutane da suka fi shiga cikin hatsari, har da mata da yara, da kuma wadanda suke cikin hatsari a nuna banbanci don, misali, naƙasa, jinsi da ra'ayin jima'i, kabila, yare, shekaru ko addini;

**I. AN AMINCE** cewa don dalilin wannan Shawarwarin, an yi amfani da waɗannan ma'anonin:

a. **Hukumar Kasa da ƙasa masu Tallafawa Cigaban Al'umma (kuma ana kiransu masu ba da kuɗin tallafi wato donors)** yana nufin hukumomin gwamnati ko wasu hukumomin jama'a ko masu zaman kansu wanda aka basu nauyin kasafta kuɗin jama'a wanda aka sani a matsayin Taimakon Cigaban Al'umma a Hukumance wato (ODA).

b. **Abokan aiwatarwa** yana nufin hukumomin gwamnati ko na jama'a, har da abokan aiki na hukumomin cigaban al'umma na ƙasa da ƙasa kamar gwamnatocin ƙasashe masu tasowa, cibiyoyin jama'a har da hukumomi na gida, manyan ƙungiyoyi masu zaman kansu da kanan kungiyoyi masu zaman kansu, jam'iyyar 'yan kasuwa, ƙungiyoyin ƙasashe daban-daban don ci gaba da taimakon agaji, da 'yan kasuwa da suke kawo kaya da ba da hidimomi a lokacin aiwatar da ayyukan jin kai ko shirye-shirye ko ƙungiyoyi masu zaman kansu da suke samun kuɗin taimakon agaji.

**II. AN AMINCE** cewa dalilin Shawarwarin DAC shine don ba da cikkaken tsari wanda zai iya goya baya, jagoranci, karfafa, da kuma taimakawa mambobin DAC da wadanda ba mambobi ba da suka bi shi (daga yanzu "Masu goyan baya wato Adherents")

a ƙarfin su a matsayin masu bada kuɗin tallafi, wasu hukumomin gwamnati da al'umma masu ruwa da tsaki na ƙasa da ƙasa don aiwatar da ƙarin cikakkun matakai mai tsari kuma an daidaita, bisa ga ka'idodin ƙasa da ƙasa da ya dace da kuma la'akari da dokokin ƙasar, wajen hana da magance SEA da SH a ayyukansu na kasafta da/ko gudanar da taimakon agaji. Wannan ya hada da sa mai tsira-da wanda aka azabtar a matakin farko, goyan bayan canza al'adun ƙungiya, horarwa, karfafa ɗaukan alhaki, da karfafa ingancin fannin taimakon agaji na ƙasa da ƙasa.

**III. ANA BA DA SHAWARAR** cewa Masu Goyon bayan sun kafa ko canza tsarurrukansu na haɗin kai don cigaba da taimakon agaji don karfafawa kariya daga SEA da SH da magancewa, magance hatsarori, da kuma taimakawa da kare mai tsira-da wanda aka azabtar. Ya kamata Masu goyon baya su ɗauki mataki don tabbatar da cewa an aiwatar da waɗannan tsarurruka ta hukumominsu na cigaban al'umma na ƙasa da ƙasa da abokan aiki a dukkan ayyukansu na kasafta kuɗi da/ko gudanar da taimakon agaji, bisa ga isasshen kayayyaki. A wajen kafa ko canza waɗannan tsarurruka, da yadda ya dace da manufofi, matsayi da nauyi, ya kamata Masu goyon baya su:

1. Kirkiro **manufofi da ka'idodin halayen ƙwarewa da neman haɓaka canje-canje ƙungiya da jagoranci a kan SEA da SH a cikin samar da taimakon ƙasa da ƙasa..** Don hakan, kamar yadda ya dace, ya kamata masu goyon baya su:

    a. Karfafa inganta **al'adu da dabi'un ƙungiya** ta mulki mai tasiri da daraja da kuma jagoranci kan manufofi, abubuwan da aka darajanta, halaye da abubuwan da ake tsammani masu alaƙa da kariya da magance SEA da SH, har da karfafa yanayin aiki da damarmaki dake shigar da kowa, babu nuna banbanci, kuma akwai daidaituwar jinsi, har da ta karfafa ɗaukan mata aiki a manyan matsayi da kara musu matsayi a dukkan ƙungiyoyin.

    b. Tabbatar da aiki mai dorewa **tare da manyan ma'aikata kuma shugabanni** su yi alƙawarin canza ko kula da al'adu da dabi'un ƙungiya na gari game da kariya daga SEA da SH da magancewa, ta tattaunawa akai-akai tare da manyan ma'aikata akan yadda za'a magance waɗannan matsaloli, da tabbatar an tanadi kayayyakin ƙungiyar don tallafawa da daidaita aiki akan SEA da SH, don gano hadin tsakanin hakkokin bil'adama gaba daya da alkawura zuwa daidaituwar jinsi.

    c. Haɗa **ka'idodi, dabaru, da tsarin aiki don kariya daga SEA da SH da magancewa** wanda ake aiwatarwa da inganci; kafa manufofi da ka'idodi; nuna wani tsarin haɗin kai; da tallafawa aiwatar da tsarin ayyukan masu alaƙa. A waɗannan ka'idodi, ya kamata Masu goyon baya su bayyana cewa babu sani babu sabo ga ƙin magance matsalolin SEA da SH, yayin da kuma kariya da magancewa ya kamata su zama bisa ga hanyar mai la'akari da mai tsira-da wanda aka azabtar wanda ke da manufar kar a cutar.

    d. Haɗa **Dokokin Aiki ko Ka'idodin Da'a** da bada ka'idodi da dokoki a bayyane don hana da magance SEA da SH, da tabbatar da jama'a na iya samu kuma ana sanar da manyan ma'aikata akai-akai a duk muhimman matakai na ɗaukan aiki (har da hanyoyin ɗaukar aiki da ladabtarwa), a lokacin shiri da aiwatar da ayyuka, a gudanar da tsarin duba ingancin aiki, da kuma abubuwan da shugabanni suka darajanta. Waɗancan dokokin da ka'idodin da'a ya kamata a turawa abokan aiki kuma a yi sanarwa sosai akai a harsuna daban-daban da ya dace da kuma tsarin da al'ummar wurin zasu fahimta.

    e. Kirkiro **dokokin ba da rahoto da mayar da martani**, tare da bayyanannen jagora ga ma'aikata kan lokacin da kuma wa za su ba da rahoto, da kuma yadda za a mayar da martani cikin sirri, mai tsira-da wanda aka zalunta da kuma ɗabi'ar da ta dace.. Ya kamata ma'aikata su san wajibin kai rahoton SEA da SH, tare da jerin lokuta don mayar da martani da tsarurrukan bibiya, kuma su san cewa akwai ka'idar dake hana ramuwar gayya, da gano cewa tsarurruka da suke inganta ɗaukan nauyi na iya jawo ƙarin kai ƙarar matsalolin SEA da SH.

    f. Hada da ka'idodi, hanyoyi, buƙatu, da/ko alkawura mai dorewa a dukkan **yarjejeniyar haɗin kai da kayayyakin kuɗi** (misali kwangila, kuɗin tallafi, yarjejeniya) tare da hanyoyin magance sabawa da buƙatun bada rahoto.

2. **Kirkirowa ko tallafawa mai tsira-da wanda aka azabtar da hanyoyin tallafi.**

Wadannan hanyoyin ya kamata su:

    a. Ba da wata **hanya mai la'akari da mai tsira-da wanda aka azabtar** zuwa kariya daga SEA da SH da magancewa, inda kuma abubuwan da mai tsira-da wanda aka azabtar suka fuskanta, hakkokinsu, buƙatunsu, da abubuwan da suke so shine a tsakiyar tsarurrukan rahotanni, bincike da tallafi, kuma da tabbatar musu ba da kuɗin tallafi da abokan aiki sun mayar da martani akan lokaci kuma sun goyi bayan kare mai tsira-da wanda aka azabtar a dukkan matakai.

Wannan hanyar ya kamata su yi la'akari musamman da waɗanda suka fi shiga cikin hatsari, har da mata da yara, da kuma mutanen da suka fi shiga cikin hatsarin nunawa banbanci bisa ga, misali, nakasa, jinsi da ra'ayin jima'i, kabila, yare, shekaru ko addini. Ya kamata a kafa tsari mai la'akari da waɗanda suka tsira da waɗanda abun ya shafa bisa ga hakkokin bil'adama, har da daraja, sirri, tsaro, da rashin nuna bambanci.

b. Hada da tsarurrukan korafe-korafe daban-daban, masu inganci, a bayyane, kuma da sauki da la'akari da mai tsira-da **wanda aka azabtar** wanda dukkan mutanen garin na iya samu, tare da buƙatu a bayyane da jagorori akan yaushe da yadda za'a yi amfani da tsarurrukan, kuma a tabbatar an yi haɗin da ya dace zuwa ga goyon bayan ba da taimako ga mai tsira-da wanda aka azabtar. Hanyoyin korafe-korafe, har da tsarin da ke cikin al'umma, ya kamata a haɗa kuma a aiwatar, a sauya bisa ga yanayin garin na musamman da al'adu, kuma a yi amfani da su tare da shugabannin garin da hukumomi inda babu matsala kuma ya dace, da kuma har yadda zai yiwu, a haɗa kai don goyon bayansa.

c. Bada tallafi hadadde kuma mai tsaro **da kariya** ga waɗanda suke kai ƙarar SEA da SH, har da mai tsira-da wanda aka azabtar, tare da haɗin kai da masu ruwa da tsaki da suka dace kamar: Majalisar Dinkin Duniya; Kungiyoyi masu zaman kansu (CSOs) da Kungiyoyin Mata na Gida; gwamnatin ƙasa da ta gida da suka dace; da cibiyoyin jama'a har da hukumomin gida. Ya kamata Masu goyon baya su shirya jagorori da mafi ƙarancin ka'idodi don taimakon mai tsira-da wanda aka azabtar magancewa da goyon baya, har da tsara muhimman masu ruwa da tsaki da masu ba da hidimomi, da kuma ta neman ba da kuɗin da ake buƙata wanda aka haɗa hannu don tallafawa zuwa mafi girman matakin da zai yiwu.

d. Nemi hanyar karfafa **hidimomi da cibiyoyin gida waɗanda akwai su da kuma daidaitawa** tare da hidimomin kare hakkin yara da cin zarafi don banbancin jinsi, da kuma magance tashin hankali akan 'yan mata inda ya dace. Ya kamata a haɗa hanya mai la'akari mai tsira-da wanda aka azabtar a dukkan ƙoƙarin karfafa magance cin zarafi don banbancin jinsi da SEA da SH a mataki na gida, har da karfafa bin doka da samun daman shari'ah. Ya kamata ƙoƙarin ya zama don karfafa ingancin da samuwar hidimomin turawa gaba da tsarurrukan kariya don rage hatsarorin ƙyamar mai tsira-da wanda aka azabtar

3. **Kafa tsarurrukan karɓar rahotannin ƙungiya da bada amsa da hanyoyin kariya daga SEA da SH.** Waɗannan tsarurrukan ya kamata su hada da:

a. **Hanyoyin korafe-korafe da bincike** waɗanda suka dace da mahallin kuma ana la'akari da waɗanda suka tsira da waɗanda abin ya shafa, kuma wanda suka hada da ayyuka da aka kafa da tsarurruka don magance matsaloli da zargi don masu ba da kuɗin tallafi da abokan aiki. Ya kamata Masu goyon bayan su yi bincike akan hanyoyi masu zaman kansu wanda ya dace, don lura cewa masu laifin da ake zargin su na da hakkin sirri su ma.

b. Hanya mai sauki, amintacciya, mai saukin yanayi, rahoto mai dacewa da al'adu **da karbar rahoto da korafe-korafe** wanda akwai sirri kuma ana boye bayanai yadda ɗai-ɗaikum mutanen da al'ummar da abin ya shafa na iya kai ƙarar abubuwan da ke faruwa, kuma wanda aka daidaita don tabbatar da Inganci a duk ƙoƙarin tallafawa. Wannan na iya hadawa da tsarurrukan fallasa masu zaman kansu don ma'aikata, abokan aiki, masu cin gajiya, da kuma iyalai da al'ummarsu, har da sauran masu ruwa da tsaki, shigar da hukumomin ƙasa da na gida inda babu matsala kuma ya dace, da kuma bisa ga tsarurrukan shariah da ƙungiyoyi na kasar.

c. **Kariya daga ramakon gayya** ga waɗanda abin ya shafa ko wadanda suka kai ƙara, har da masu fallasa, ta samar da ka'ida don kariya daga ramakon gayya.

d. Tallafawa **kwarewar 'yan gari, bin dokoki, samun damar shariah, da kuma ƙara ɗaukan nauyi,** ta haɗin kai wajen taimakon cigaba da na agaji, gwargwadon yanayin yankin.

e. Karfafa da bayyana **hanyoyin karbar rahoto da bincike** don tabbatar da ɗaukan alhaki a cikin gida da waje, tallafawa kariya da ƙarin samun damar bayanai, da la'akari da tsaron, buƙatu, hakkoki da abubuwan da waɗanda suka tsira da waɗanda abin ya shafa suke so bisa ga samun bayanai, sirri, bada izini, da binciken hatsari, don kare wanda ya tsira da wanda abin ya shafa da kuma manufar hana faruwarsa a gaba.

f. Ka'idodi da hanyoyi don tabbatar da duk **tsarurrukan da nauyin manyan ma'aikata** don tabbatar da ɗaukan nauyi ga ma'aikata idan ya zama dole, har da kora daga aiki, dakatarwa daga aiki na ɗan wani lokaci, da wasu matakai na gudanarwa. Sannan, **abubuwan sakayya ta gari don karfafa dabi'u masu kyau** kuma ya kamata a yi amfani da

lambar yabo don samar da al'ada ta shigar da kowa, aminci, da aiki a bayyane don karfafa ɗaukar nauyi da nuna gaskiya.

g. Tsarurruka da aka bayyana don magance **rashin hukunta masu laifuka**, da **hukunci** ga ma'aikatan da suka sabawa dokokin aiki.

h. Gudanar da ingantaccen tsarin **ɗaukar aiki da duba ingancin aiki mai nuna gaskiya, da kuma hanyoyin turawa gaba** don hana ɗaukan (misali kara ɗaukan aiki, tura wani wuri, ko kara matsayi) masu laifi har da ingantaccen tsari don duba tarihin masu neman aiki, inda suka yi aiki a baya, da bayanan laifukan da suka taɓa yi a baya.

4. **Gudanar da horo, wayar da kan jama'a, da sadarwa a kan kariyar SEA da SH.** Waɗannan matakan suna buƙatar wadataccen ci gaba mai wadatarwa kuma ya kamata ya haɗa da:

a. Sadarwa mai inganci don jawo hankalin al'umma akan magance SEA da SH, har da bada bayanai akan: dokokin kasa da ya dace, ka'idodin hukuma mai ba da kuɗin tallafi, da dokokin aiki; buƙatu da halayen da manyan masu bada kuɗin tallafi suke tsammani daga ma'aikata, abokan aiki, har da fannin kamfanoni; da kuma yadda za'a iya amfani da hanyoyin korafe-korafe don kai ƙarar sabawa dokoki.

b. **Horarwa akai-akai da karfafa ilimi** don manyan ma'aikata da sauran ma'aikata akan ka'idodi, dokokin aiki, hanyoyin kai korafe-korafe da bada rahoton rashin da'a, da kuma sakamakon sabawa ka'idodi, har da ka'idodin hana fansa, don tabbatar da canjin al'adu mai tasiri da kuma karfafa muhallin aiki inda akwai tsaro, kwarin gwiwa da darajanta juna. Horarwa da haɓaka iya aiki ya kamata a haɗa su, ko kuma daidaita su da, horon daidaito tsakanin maza da mata da haɓaka ƙarfin aiki.. Inda zai yiwu, a zaɓi ma'aikata musamman don kariya daga SEA da SH kuma ya kamata su samu horo na kwarewa.

c. **Ayyukan wayar da kan jama'a da kokarin ilimantarwa, da ƙoƙarin kariya** ko shirye-shirye tare da abokan aiki don tabbatar masu karbar taimako da jama'a suna sane game da hakkokinsu, hanyoyin kai rahoto, da hidimomin taimako dake samuwa. Ya kamata a tuntubi masu cin gajiyar taimakon agaji da jama'a na gida a lokacin tsara shirye-shiryen SEA da SH, da kuma tsare-tsare gaba-daya inda ya dace, don tabbatar an biya buƙatunsu. Wannan na iya karfafa ilimi da horarwa ga ƙungiyoyin da aka kafa na gida, har da ƙungiyoyin hakkokin mata, da kuma cibiyoyi da tsarurrukan kariya daga SEA da SH da suke cikin ƙasar. Ya kamata a rika musayar kayayyaki tsakanin babban ofishi (hedkwata), kananan ofisoshi , abokan aiki, da gwamnatin kasar da na gida, har da cibiyoyin jama'a har da hukumomin gida, inda babu matsala kuma ya dace; game da daidaituwar jinsi da rashin nuna banbanci, don hana da bada kariya daga SEA da SH.

5. **Tabbatar da daidaituwa na ƙasa da ƙasa ga kariya da tallafin SEA da SH.** Don haka, Ya kamata Masu goyon baya su:

a. **Daidaita na ƙasa da ƙasa** tare da masu ba da gudummawa da abokan hulɗa masu aiwatarwa don saita cikakkun mizanai da tsammanin, daidaita daidaitattun matakan da ake da su gwargwadon yadda zai yiwu, da tallafawa buƙatun waɗanda suka tsira da waɗanda abun ya shafa, da kuma ɗaukan cikkaken matakai wajen kariya da magance SEA da SH.

b. **Hada da alkawuran da akwai** daga wasu mambobin DAC matsayin tushen ka'ida don ɗaukan mataki akan kariya da tallafawa, har da Muhimman Ka'idodin Aikin Agaji akan Inganci da Ɗaukan Alhaki (CHS), Mafi Karancin Ka'idodin Aiki na Kwamitin Mai Jagorantar Kungiyoyin Agaji (MOS-PSEA), Shawarwarin OECD da DAC da ya dace har da sauran alkawuran kasa da kasa, har da Alkawuran da masu ba da kuɗin tallafi suka yi don magance ci da gumi da cin zarafi da tursasawa ta hanyar jima'i a fannin taimakon agaji na ƙasa da ƙasa a Taron Kariya da aka yi a London a shekarar 2018.

c. Tabbatar an kara **haɗin kai tsakanin mambobin DAC, abokan aiki da kwararru na duniya da na ƙasar** akan kariya da magance SEA da SH; UN, musamman Kwamiti mai Jagorantar Kungiyoyin Agaji (IASC); da Mashawartar Masu Daidaita Tsarin UN wato UN System Chief Executives Board for Coordination (CEB). Ya kamata a yi ƙoƙari musamman don daidaita ka'idodi don tallafawa waɗanda suka tsira da waɗanda abun ya shafa, gudanar da bincike, da ba da rahotanni daga abokan aiki.

d. Goyi bayan shirya matakai don duba ƙoƙarin **kungiyoyi da suke aiki a ƙasashe daban-daban** game da tsarin su ga SEA da SH, kamar waɗanda ake kan shiryawa daga Cibiyar Binciken Koƙarin Kungiyoyi na kasashe daban-daban

(MOPAN).

e. **Samar da kayayyaki** – har da kuɗi da ma'aikata – don cimma manufofin wannan Shawarar ta DAC da kuma tabbatar cewa abokan aiki na iya bin wadannan ka'idodin.

6. **Samar da hanyoyi don lura, kimantawa, da rahotanni akan kariya da magance SEA da SH.** Don haka, Ya kamata Masu goyon baya su:

a. Kafa tsarurruka don **lura da bitar** ayyukan magancewa, goyan baya, da bibiya, kamar bincike akan cigaba da aka samu da tasiri, kimantawa, ko hanyoyin bita akan dabi'u mafi kyau da abubuwan da aka koyo, da kuma ma'anonin sannanun abubuwa.

b. Inganta **bayanai da ake tattarawa, har da bayanin jinsi da shekaru a rabe,** matakan samun bayanai da kididdiga, da bincike-bincike da kimanta ayyukan hukumomi da abokan aikinsu da cewa an tabbatar da sirri ga masu tsira, waɗanda abin ya shafa da ƙungiyoyin mutanen da suka fi shiga cikin hatsari. Waɗannan ƙokarin na iya hada da raba bayanai bisa ga shekaru da jinsi don iya amfani dashi a ƙungiyoyi, wurare da lokuta daban-daban don koyo da gano yanayin da zai sa a gano matsaloli a wasu ɓangarori.

**IV. NA GAYYATAR** Babban Sakataren UN ya wallafa wannan shawarar DAC;

**V. NA GAYYATAR** Masu goyon baya su wallafa wannan Shawarar DAC, musamman ta hukumominsu na cigaba, taimakon agaji, da neman zaman lafiya da abokan aikinsu da kuma duk gwamnatoci;

**VI. NA GAYYATAR** waɗanda ba sa goyon baya su yi la'akari kuma su bi Shawarar DAC;

**VII. NA KARFAFA** abokan aiki na ƙungiyoyi masu zaman kansu, 'yan kwangila, da waɗanda suke samun kuɗin tallafi su wallafa kuma su bi wannan Shawarar DAC;

**VIII. BADA UMURNI GA** Cibiyar DAC akan Daidaituwar Jinsi su:

a. Goyi bayan dandalin masu ruwa da tsaki daban-daban inda Masu goyon baya, ta wani tsarin tattaunawa, za su ba da ka'idodi, dabi'u mafi kyau, da hanyoyin fasaha ga kariya daga SEA da SH da tallafawa don taimakawa da koyo daga juna da sauyi, da kuma samar da kayan aiki don aiwatar da wannan Shawarar DAC;

b. Lura da koyi aiwatar da wannan shawarar DAC, har da ta tsarin sake duba takwarori na DAC, da yarjejeniyar ƙasa da ƙasa da suke dacewa, kamar na mata, zaman lafiya da tsaro, da haɓaka zaɓuɓɓuka don sa ido da bita akai-akai, a cikin farkon shekaru biyar don ba da dama da goyon baya don koyon darasi, daidaitawa, da raba kyawawan ayyuka don gina fahimta da iyawa;

c. Sannan ba da rahoto zuwa DAC kafin shekaru biyar bayan bin wannan Shawarar DAC kuma daga baya akalla bayan kowane shekaru goma.

## Asalin bayanai

***Haɗin Kai don Shawo kan Cutarwa, Cin Zarafi da Tursasawa ta hanyar Jima'i***

Shawarar Kwamiti akan Taimakon Ci-gaba wato Development Assistance Committee (DAC) Recommendation akan Cutarwa, Cin Zarafi da Tursasawa ta hanyar Jima'i a lokacin Haɗin Kai don Ci-gaba da bada Taimakon Agaji: An amince da Muhimman Ginshikin Kariya da Tallafi a ranar 12 ga watan Yuli 2019.

Shawarar DAC shine farkon kayan aiki na ƙasa da ƙasa akan cutarwa da cin zarafi ta hanyar jima'i (SEA) da tursasawa ta hanyar jima'i (SH) wanda ya shafi haɗin kai don ci-gaba da taimakon agaji. An shirya ne domin rahotanni masu ban mamaki da ake samu akan ci da gumi da cin zarafi a lokacin haɗin kai don ci-gaba da taimakon agaji kuma yana ba da cikakken tsari don tallafawa, jagoranta, da sakawa da kuma taimakon gwamnatoci - a matsayin su na masu ba da kuɗin tallafi, hukuma, da masu ruwa da tsaki na ƙasa da ƙasa - don aiwatar da ƙarin matakai masu dacewa da juna kuma an daidaita, da bin ka'idodin ƙasa da

ƙasa, don hana da magance SEA da SH a ayyukansu a lokacin kasafta da/ko gudanar da taimakon agaji, har da sa waɗanda suka tsira da waɗanda abin ya shafa a matakin farko, tallafawa sauye-sauyen al'adu na kungiya, karfafa ilimi, karfafa ba da lissafi, da karfafa mutuncin sashen ba da agaji na kasa da kasa.

Shawarar DAC yana da manufar zama wani babban ka'ida don gina tsarurruka mafi kyau don hana da magance SEA da SH kuma yana bisa ginshiki guda shida: (i) Ka'idodi, sharuddan halaye a wajen aiki, canjin ƙungiya da mulki; (ii) Tsarurruka masu la'akari da Waɗanda suka tsira/waɗanda abun ya shafa; (iii) Tsarin karbar rahotanni na ƙungiya da mayar da amsa da hanyoyin; (iv) Horarwa, jawo hankalin jama'a da sadarwa; (v) Daidaita aiki na ƙasa da ƙasa; da kuma (vi) lura, kimantawa, da koyo daga juna da ba da rahoto.

Bugu da kari, Shawarar DAC ya hada da abubuwan da ke da manufar goyan bayan mambobin DAC da waɗanda ba mambobi ba amma suna bin shi a ƙoƙarin su na aiwatar da alƙawuran da ya ƙunsa, ƙafa tsarurruka don cigaba da koyo, da sa ido akan nasarar da aka samu. Zai buƙaci sa hannun jari isasshe wajen samar da kayayyaki da bincike don karfafa dabi'u mafi kyau na ƙasa da ƙasa a gaba, da la'akari da bukatar magance rashin daidaituwar iko da jinsi wanda sune tushen wadannan matsalolin.

Duk da yake Shawarwarin DAC ba ya neman cikakken ma'anar SEA da SH, wasu majiyoyi na iya samar da jagora mai amfani don yaɗuwa, fassara, da aiwatarwa.

Misali, wasu sanarwa da Sakatare Janar na Majalisar Dinkin Duniya ya fitar - waɗanda suka shafi ma'aikatan Majalisar Dinkin Duniya da nufin hanawa da magance lamuran lalata da cin zarafin mata a tsarin Majalisar Dinkin Duniya - ya shafi "cin da gumi ta wurin jima'i" da "cin zarafi ta wurin jima'i".Musamman, sanarwa ST/SGB/2003/13 wanda yace ci da gumi ta hanyar jima'i yana nufin “kowane ainihin ko ƙoƙarin cin zarafi daga wani ma'aikacin dake matsayin hatsari, bambancin iko ko aminci don dalilin jima'i, har da amma ba iyakance, samun riba na ɗan lokaci, ta matsayi ko siyasa da cutar da wani ta hanyar jima'i.” “Ci da gumi ta hanyar jima'i” don haka wani babban kalma ne wanda ya hada da, misali musaya jima'i, neman musaya jima'i, da dangantakan da wani ya fi iko. Game da “cin zarafi ta hanyar jima'i”, wancan mujallar ya ba da ma'ana cewa kalmar na “nufin ainihin ko barazanar kai hari zahiri da ya shafi jima'i, ko ta tilastawa ko cikin yanayin rashin daidaituwa ko dole ”.

Game da “tursasawa ta hanyar jima'i”, Babban Taron Majalisar Dinkin Duniya 'Inganta kokarin hanawa da kawar da duk wani nau'i na cin zarafin mata da' yan mata: tursasawa ta hanyar jima'i,' (A/RES/73/148) ya jaddada cewa tursasawa ta hanyar jima'i “ya ƙunshi cigaban halaye da ba'a amince da su ba kuma ba'a martaba ba da dabi'u da suka shafi jima'i wanda na iya hada da amma ba a iyakance shi ba, ba da shawarwarin jima'i ko neman jima'i, neman alfarmar jima'i da magana, nuna ko halayen da suka shafi jima'i wanda da dalili ake ganinsa a matsayin cin fuska ko wulakanci.”

Na ƙarshe inda kalmar "yara" an yi amfani dashi a Shawarar DAC, mambobin DAC sun yi la'akari da Yarjejeniyar Majalisar Dinkin Duniya akan Hakkokin Yara, wanda ya ba da ma'anar "yara" a matsayin kowane mutum dake kasa da shekaru 18.

Tsarin aiki mai haɓaka don Bada Shawarwarin DACA watan Yunin 2018, DAC ta kafa Rukunin bincike na DAC akan PSEA, wanda wakilai daga Austria, Ireland da Ingila suka jagoranta.. Rukunin binciken sun hada da, mambobin DAC da aka zaba, wakilai da sauransu, Majalisar Dinkin Duniya da Kwamitin mai Jagorantar Kungiyoyin Agaji, Bankin Duniya, Cibiyoyin da suke wakiltar kungiyoyi masu zaman kansu, da mambobi daga ƙasashe da babu DAC.

Rukunin binciken sun yi aiki tare da Kungiyoyi masu zaman kansu (CSOs), bisa ga tsarin DAC-CSO akan Hulda, don taimakawa wajen tabbatar da cewa Shawarar DAC zai taimaka wa duk mambobin DAC da abokan aiki wajen daidaita ayyunkansu akan hana da daukan mataki a kan SEA da SH. Kuma Rukunin binciken sun yi aiki tare da bayani daki-daki akan dabi'un mambobin DAC wajen hana da daukan mataki a kan SEA da SH wanda aka tattara ta bincike mai zurfi da aka turawa mambobin DAC a shekara 2018.

***Lura akan aiwatarwa, yadawa da bin tsarin***

Cibiyar DAC akan Daidaituwar Jinsi (GENDERNET) za ta lura da aiwatarwa ta hanyar tsarin sake duba takwarorin na DAC da yake akwai su, tare da samar da zabin don yawan lura da kuma yin bita a cikin shekaru biyar na karbar shawarar DAC. GENDERNET za ta ba da rahoto game da aiwatarwa ga DAC ba da daɗewa ba bayan shekaru biyar bayan karɓar ta kuma akalla kowace shekara goma bayan haka